# ABUBUWAN DA SUKE WARWARE MUSULUNCI

Hausa



**Wallafar**
**BABBAN MALAMI**
**SHEIKH MUHAMMAD BIN ABDUL WAHHAB**
**DA HARSHEN HAUSA**
**TARJAMAR**
**SHEIKH AMEEN AL- DEEN ABUBAKAR**

COOPERATIVE OFFICE FOR CALL
AND GUIDANCE EASTERN JEDDAH
.BOX: 102137-JEDDAH21321K.S.A. TEL: 6200005(5 LINES)-FAX: 6240398

# ABUBUWAN
# DA SUKE WARWARE
# MUSULUNCI

Daga Littattafan Da Ma'aikatar Harkokin Addinin
Musulunci, Da Waƙafai, Da Kuma Wa'azi Da
Shiryarwa Ta Buga

# ABUBUWAN DA SUKE WARWARE MUSULUNCI

Wallafar
BABBAN MALAMI
SHEIKH MUHAMMAD BIN
ABDULWAHHAB

Da Harshen Hausa

Tarjamar
SHEIKH AMEEN AL-DEEN ABUBAKAR

Offishin Buga Takardu Da Yaɗasu Na Ma'aikatar
Suka Ɗauki Nauyin Kulawa Da Bugunsa

1418 AH

ⓒ وزارة الشئون الإسلامية والأوقاف والدعوة والإرشاد ، ١٤١٨هـ

*فهرسة مكتبة الملك فهد الوطنية أثناء النشر*

محمد بن عبدالوهاب بن سليمان

نواقض الإسلام - الرياض.

٢٤ ص ، ١٣ × ١٠سم

ردمك : ٢-١٣٣-٢٩-٩٩٦٠

( النص بلغة الهوسا )

١-التوحيد ٢-الإسلام ٣-الوعظ والإرشاد أ- العنوان

ديوي ٢٤٠ ١٨/٠٤١٨

رقم الإيداع : ١٨/٠٤١٨

ردمك : ٢-١٣٣-٢٩-٩٩٦٠

# GABATARWA

Wannan ɗan littafi yana da muhimmanci kowane musulmi, namiji da mace, su karanta shi, saboda amfaninsa, musamman game da sha'anin gyara aƙidah. Yau saboda jahiltar addini, mutane da yawa suna aikata abubuwa daban-daban wadanda za su ruguza imaninsu, ba tare da sun sani ba. Domin haka bayyana "abubuwan da suke warware Musulunci" ya zama larura ga mutane a yau.

Ƙungiyar "Jama'ah Al-Da'awah fi Nigeria" babban burinta ne ta

gabatar da wannan ɗan littafi ga masu jimirin raya Sunnah da kyautata Aƙidah. Allah Ta'ala Ya kuma yi mana jagora wajen aiki da Alkur'ani da Hadisi, amin.

**WASSALAM**


Sheihk Ameen Al-Deen Abubakar,
Jama'ah Al- Da'awah Fiy Nigeria,
Ofishin Al-Maktaba Al-Salafiyya,
483, Sulaiman Crescent,
P. O. Box 6118,
**KANO, NIGERIA.**

# BISMILLAHIR-
# RAHMANIR- RAHIM

## *ABUBUWAN DA SUKE WARWARE MUSULUNCI*

Ya ɗan uwa Musulmi, dole ne ka san cewar akwai abubuwan da aikatasu yake warware Musulunci (idan ka yi ɗayansu ka fita daga addinin Musulunci ke nan, Allah Ya kiyaye). Mafi afkuwa daga cikin waɗannan abubuwa guda goma ne, lallai ne ka guje su.

## *NA ƊAYA*

Tarayya a cikin bautawa Allah. Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce:

﴿ إِنَّهُۥ مَن يُشْرِكْ بِٱللَّهِ فَقَدْ حَرَّمَ ٱللَّهُ عَلَيْهِ ٱلْجَنَّةَ وَمَأْوَىٰهُ ٱلنَّارُ ۖ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنْ أَنصَارٍ ﴾

« Haƙiƙa, duk wanda ya yi tarayya (shirka) da Allah, Allah Ya haramta masa Aljanna, kuma makomarsa Wuta; kuma azzalumai babu waɗansu mataimaka a gare su ».

Kiran matattu da addu'a da neman taimako daga gare su, da yi musu bakance ko yanka, duk fanni ne na shirka.

## *NA BIYU*

Duk wanda ya sanya tsani tsakaninsa da Allah (kamar Mala'iku, Annabawa, Waliyyai, ko wasu abubuwa) da mutum zai rika kira da addu'a, yana neman su cece shi, yana dogara a kansu, to mai aikata haka ya kafirce, kamar yadda dukkan Malamai suka tabbatar.

## *NA UKU*

Duk wanda bai kafirta masu aikin shirka ba, da wanda yake shakkar kafircinsu, ko kuma yake inganta

hanyarsu, (duk mai haka) shi ma ka sani ya zama kafiri.

## *NA HUDU*

Duk wanda ya yarda da wata shiriya ba ta Annabi, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ba, kuma ya ɗauka wannan shiriya tafi ta Ma'aikin Allah cika, ko kuma ya ɗauka cewar hukuncin wani daban yafi hukuncin Ma'aikin Allah kamar waɗanda suke fifita hukuncin gumaka (kamar gwamnatocin zamani waɗanda ba su yarda da shiriyar Annabi Muhammad, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ba, duk

wanda ya yarda da haka ya zama kafiri.[1]

---

[1] Ga misalai na: kamar haka:

(a)- Ɗaukar cewa tsare-tsare da dokokin da mutane suke shiryawa da hannayensu, sun fi Shari'ar Musulunci.

Ko kuma ɗaukar Addinin Musulunci ba zai dace a yi amfani da shi ba a ƙarni na ishirin (a zamanin yau).

Ko kuma cewa Musulunci ne sababin rashin ci gaban Musulmi. Ko kuma ɗaukar alaƙar mutum da Allah (da harkokin addini) abu ne da ya shafi mutum shi kaɗai, bai shafi sauran harkokinsa na rayuwa ba (wato kamar dai yadda wasu suka ɗauka, tsarin

addinin mutum ba shi da alaƙa da harkokin duniya na yau da kullum).

(b)- Maganar da ake cewa wai zartar da hukuncin Allah kamar yanke hannun ɓarawo, ko jefe mazinaci wanda yake da aure, a ce wai haka bai dace da zamanin da muke ciki ba.

(c)- Ɗaukar cewar ya halatta a yi hukunci ba da abin da Allah Ya saukar ba, a cikin mas'alolin shari'a, da laifukan da suke bukatar tsayar da haddi, da wasunsu, ko da mutum bai yarda da cewa hukuncin wanin Allah ya fifici hukuncin Allah ba, saboda kawai halattawa (bada dama) a yi hukunci da wata doka da ba ta Allah ba, to .yin haka halattawa ne ga abin da Allah Ya haramta, kamar yadda dukkan malamai suka faɗa. Duk kuwa wanda ya halatta abin da Allah Ya haramta, wanda

## *NA BIYAR*

Duk wanda yake ƙin abin da Manzo, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya zo da shi, wato ya ƙi yarda da halaccin abin ko da yana aiki da shi, to wannan mutum ya zama kafiri, saboda faɗin Allah Madaukakin Sarki:

---

da an faɗa kowa ya san haramun ne a addini, kamar zina da shan giya, da cin riba, da yin hukunci ba da abin da Allah Ya saukar ba, duk wanda ya yi haka kafiri ne kamar yadda dukkan musulmi suka tabbatar da haka.

﴿ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ كَرِهُوا مَا أَنزَلَ اللَّهُ فَأَحْبَطَ أَعْمَالَهُمْ ﴾

« Wannan, saboda lallai su, sun ƙi abin da Allah Ya saukar, domin haka Ya ɓata ayyukansu ».

## *NA SHIDA*

Duk wanda ya yi isgilanci da wani abu na daga addinin Ma'aiki, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ko ya yi isgilanci da lada ko uƙubar da addinin ya faɗa, shima wannan ya kafirta. Saboda Allah Maɗaukakin Sarki Yana cewa:

﴿قُلْ أَبِاللَّهِ وَءَايَٰتِهِۦ وَرَسُولِهِۦ كُنتُمْ تَسْتَهْزِءُونَ ۞ لَا تَعْتَذِرُوا۟ قَدْ كَفَرْتُم بَعْدَ إِيمَٰنِكُمْ﴾

« Ka ce: shin da Allah, da kuma ayoyinSa da ManzonSa kuka kasance kuna yin izgili? Kada ku kawo wani hanzari, haƙiƙa kun riga kun kafirta bayan imaninku ».

## *NA BAKWAI*

Aikata sihiri, wanda a cikinsa har da na raba masoya, kamar a jefa wa miji ƙin matarsa; ko kuma da aikin mallakewa, wato a san yadda za a

sa mutum ya so abin da ba ya so ta hanyar sihiri (bokanci), duk wanda ya aikata ɗaya daga ciki, ko ya yarda da shi, ya kafirta. Saboda Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce:

﴿ وَمَا يُعَلِّمَانِ مِنْ أَحَدٍ حَتَّىٰ يَقُولَآ إِنَّمَا نَحْنُ
فِتْنَةٌ فَلَا تَكْفُرْ ﴾

« Su (Mala'ikun guda biyu, Harut da Marut) ba su koya wa wani (sihiri) ba, ba tare da sun gaya masa (maganar kashedi) ba, "hakika, mu fa fitina (wato jarabawa) ce kawai, don haka kada ka kafirta" ».

## *NA TAKWAS*

Ba wa mushrikai goyon baya, da ba su taimako a kan musulmi, shi ma kafirci ne, saboda Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce:

﴿ وَمَن يَتَوَلَّهُم مِّنكُمْ فَإِنَّهُۥ مِنْهُمْ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴾

« Duk wanda ya jiɓince su daga cikinku, to lallai ne shi ma yana daga cikinsu; haƙiƙa Allah ba ya shiryar da azzaluman mutane ».

## *NA TARA*

Duk wanda ya yarda cewa wasu mutane an yi musu izinin kauce wa shari'ar Annabi Muhammad, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya zama kafiri; kamar yadda Allah Maɗaukakin Sarki Ya faɗa:

﴿ وَمَن يَبْتَغِ غَيْرَ ٱلْإِسْلَٰمِ دِينًا فَلَن يُقْبَلَ مِنْهُ وَهُوَ فِي ٱلْآخِرَةِ مِنَ ٱلْخَٰسِرِينَ ﴾

« Duk wanda ya ke neman wanin Musulunci ya zama addini, to ba za a karɓa daga gare shi ba, kuma a Lahira yana daga cikin waɗanda suka yi hasara ».

## NA GOMA

Bijirewa addinin Allah gaba ɗaya, ko bijirewa abin da Musulunci ba ya ingantuwa sai da shi, mutum ya ce ba zai koyi wannan abin ba, ko kuma ba zai yi aiki da shi ba, yin haka ma kafirci ne. Saboda Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce:

﴿ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن ذُكِّرَ بِـَٔايَـٰتِ رَبِّهِۦ ثُمَّ أَعْرَضَ
عَنْهَآ ۚ إِنَّا مِنَ ٱلْمُجْرِمِينَ مُنتَقِمُونَ ﴾

« Kuma wa ya fi zalunci (mugun aiki) sama da wanda aka tunatar da shi ayoyin Ubangijinsa, sa'an nan ya bijire musu; haƙiƙa Mu masu

ɗaukar fansa ne daga masu laifi (mujirimai) ».

Kuma Allah Ta'ala Ya ce:

﴿ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ عَمَّآ أُنذِرُوا۟ مُعْرِضُونَ ﴾

« Kuma wadanda suka kafirta, masu bijirewa ne daga abin da aka yi musu gargaɗi da shi ».

Babu wani bambanci ga wanda ya aikata ɗaya daga cikin waɗannan abubuwa da suke warware Musulunci, da wasa yake yi, ko da gaske yake yi. Ko kuma saboda tsoro, amma banda wanda aka tilasta.

Muna neman tsari da Allah daga aikata duk wani abin da zai jawo fushinSa da matsananciyar azabarSa.

Sheikh Ameen Al-Deen Abubakar,

Jama'ah Al-Da'awah Fiy Nigeria.

27-3-1404 A. H.

1-1-1984 A. D.

من مطبوعات وزارة الشئون الإسلامية والأوقاف والدعوة والإرشاد

# نواقض الإسلام

تأليف الإمام الشيخ
محمد بن عبد الوهاب

بلغة الهوسا

ترجمة
الشيخ امين الدين أبوبكر

أشرفت وكالة شئون المطبوعات والنشر بالوزارة على إصداره
عام ١٤١٨ هـ